Hausa - Zabura - Praying WP Psalms

Zabura 68:1 Da ma Jehovah ya tashi ya warwatsa maƙiyansa! Da ma su waɗanda suke ƙinsa su gudu!

Zabura 5:9,10 Abin da maƙiyana suke faɗa, Ba abin da za a yarda da shi ba ne, Su dai, so suke su hallakar kawai, Bakinsu kamar buɗaɗɗen kabari yake, Maganganunsu kuwa suna da taushi da kuma yaudara. 10 Ka kāshe su, ka hukunta su, ya Jehovah Ka watsar da mugayen shirye-shiryensu, Ka kore su daga gabanka sabili da yawan zunubansu, Da kuma tayarwar da suke yi maka.

Zabura 11:6 akan aukar da garwashin wuta Da kibritu mai cin wuta a kan mugaye, Yakan hukunta su da harshen wuta mai ƙuna.

Zabura 18:14 Ya harba kibansa, ya watsa magabtana, Da walƙiya ya kore su.

Zabura 18:17 a cece ni daga magabtana masu ƙarfi, Daga kuma dukan masu ƙina, Gama sun fi ƙarfina!

Zabura 18:39 Kakan ba ni ƙarfin yin yaƙi, Kakan ba ni nasara a kan magabtana.

Zabura 18:45 Za su karai, Su fita, suna rawar jiki daga kagaransu.

Zabura 27:11 Ka koya mini abin da ya kamata in yi, ya Ubangiji, Ka bi da ni kan lafiyyiyar hanya, Domin ina da magabta da yawa.

Zabura 35:1-8 Ka yi hamayya da masu hamayya da ni, ya Ubangiji, Ka yi faɗa da masu faɗa da ni! 2 Ɗauki garkuwa da makamanka, ka zo ka taimake ni. 3 Ka daga mashin yaƙinka sama, da gatarinka, Ka yi gaba da masu fafarata. Ka faɗa mini kai ne Mai Cetona! 4 Ka sa a kori waɗanda suke ƙoƙari su kashe ni, a kunyatar da su! Ka sa waɗanda suke mini maƙarƙashiya su juya da baya, su ruɗe! 5 Ka sa su zama kamar tattakar da iska take kwashewa, Kamar waɗanda mala'ikan Ubangiji yake korarsu! 6 Ka sa hanyarsu ta duhunta, ta yi santsi, A sa'ad da mala'ikan Ubangiji yake fyaɗe su ƙasa! 7 Suka kafa mini tarko ba dalili, Sun kuma haƙa rami mai zurfi don in faɗa ciki. 8 Amma kafin su farga, hallaka za ta kama su. Tarkunan da suka kafa za su kama su, Su kuma fāɗa cikin ramin da suka haƙa!

Zabura 52:5 Don haka Jehovah zai ɓata ka har abada, Zai kama ka, ya jawo ka daga alfarwarka, Zai kawar da kai daga ƙasar masu rai.

Zabura 60:12 Idan Jehovah yana wajenmu, Za mu yi nasara, Zai kori abokan gābanmu.

Zabura 66:3 Ku faɗa wa Jehovah cewa, “Al'amuran da kake aikatawa Suna da banmamaki ƙwarai! Ikonka yana da girma ƙwarai, Har maƙiyanka sukan durƙusa a gabanka don tsoro.
Zabura 68:35 Jehovah al'ajabi ne a tsattsarkan wurinsa, Jehovah na Isra'ila! Yana ba da ƙarfi da iko ga jama'arsa. Ku yabi Jehovah!
Zabura 70:1 Ka cece ni, ya Jehovah! Ya Ubangiji, ka yi hanzari ka taimake ni!
Zabura 71:13 a sa a kori waɗanda suka tasar mini, A hallaka su! Ka sa a kunyata waɗanda suke ƙoƙari su cuce ni, A wulakanta su sarai!
Zabura 76:12 Yakan ƙasƙantar da shugabanni masu girmankai, Ya tsoratar da manyan sarakuna.
Zabura 118:10 Maƙiya da yawa sun kewaye ni, Amma na hallaka su ta wurin ikon Ubangiji!
Zabura 118:12 Suka rufe ni kamar ƙudan zuma, Amma suka ƙone nan da nan kamar wutar jeji, Ta wurin ikon Ubangiji na hallaka su!
Zabura 149:8,9 Su ɗaure sarakunansu da sarƙoƙi, Su ɗaure shugabanninsu da sarƙoƙin baƙin ƙarfe, 9 Su hukunta wa al'ummai, kamar yadda Jehovah ya umarta. Wannan shi ne cin nasarar jama'ar Jehovah! Yabo ya tabbata ga Ubangiji!

Pastor T. John Franklin
Church of Salvation, Healing, and Deliverance
COS-HAD.org